

**SHIRIN SADUWAR DA MUTUM BA YA IYA KAUCE WA**

A fili yake a cikin Littafi Mai Tsarki a Ibraniyawa sura 9:27 cewa, da yake fa an kudurta wa mutane su mutu sau daya, baya wannan sharia. Wannan shirin Allah game da mutane ya kunsa ababe biyu: (i) Dole ne mutane zasu mutu (ii) Dole ne kuma a yi masu sharia.

Mutuwar mai bin Kristi abu mai daraja ne a ganin Ubangiji Zabura sura 116:15 amma Ubangiji ba ya jin dadi cikin mutuwar mugu ba Ezekiel sura 33:11 mugayen anan sun kunsa dukanin wanda sun ki karban Yesu ya zama Ubangijin su, da mai cetonsu a lokacin rayuwar su. Dukanin wanda sun mutu cikin wannan hali rashin ba da gaskiya ga Isa Almasihu, za a tashe su daga matatu domin su fuskanci sharia Allah a gaban babban farin kursiyi. Duba Ruya ta Yohanna sura 20:11-15. (Na ga kuma babban farin kursiyi, da wanda ke zaune a bisansa, wanda sama da kasa suka guje ma fuskansa; ba a ko samu masu wuri ba, Na ga matatu kuma, kanana da manya, suna tsaye a gaban kursiyin, aka bude Litattafai; aka bude wani Littafi kuma, Littafi rai ken nan: Aka yi wa matatu sharia kuma bisa ga abin da aka rubuta cikin Litattafai, gwargwadon ayyukansu... Kuma wanda aka iske ba a rubuta shi cikin Littafin rai ba, aka jefar da shi cikin korama ta wuta. Mutuwa ta biyu kenan, Ko baka sani ba ana daukan rohoton rayuwar ka? Ko baka sani ba ayyukan ka na siri da zunuban da kake aikatawa ana daukan rohotonsu a cikin Litattafai da za a bayana su a ganin idon kowa a ranar sharia? Bayan da aka yi wa marasa ceto maza da mata sharia daga cikin ayyukansu a Litattafai, aka bude wani Littafi kuma, **LITTAFIN RAI.** Abayane yake a cikin Littafin Mai Tsarki cewa duk wanda ba a iske shi a rubuce a wannan **LITTAFIN RAI** ba, za a jefar da shi a korama ta wuta, Kana so ka karasa a cikin korama ta wuta ne? In da Littafi Ishaya sura 66:24 ya bayana cewa, wutarsu kuma ba za a bi ce ta ba, tsutsarsu ba za ta mutu ba?

Littafi Mai Tsarki ta gaya mana game da wannan sharia mai ban tsaro ga marasa ba da gaskiya ga Isa Almasihu domin ba su dama ce ta kaurace wa wannan sharia mai zuwa. Ibraniyawa sura 2:3 yace “Kaka zamu tsira idan mun kyale ceto irin wannan maigirmma? wanda a ka fara fadinsa ta wurin Ubangiji, kana aka karfafa shaidarsa a gare mu ta bakin wandanda suka jishi.

Ka tuna, babu mai bin Kristi na gaske da za ya tsaya-gaban Allah a babbanfarin kursiyin. Wannan mumuman sharia na jira dukanin wandanda suka ki karbi Isa Almasihu daya zama Ubangijinsu da mai cetonsu. A cikin Yohanna sura 3:17-18, a bayane yake cikin Littafi Mai Tsarki cewa, Allah ya aiko Dan sa ba domin yayi wa duniya sharia ba amma duniya ta tsira ta wurin sa. Wanda yana bada gaskiya gare shi ba a yi masa sharia ba: wanda bai bada gaskiya ba an rigaya an yi masa sharia, domin bai bada gaskiya ga sunan Da haifaffe kadai na Allah ba.
Hanya daya ce wanda zaka iya tsira daga sharia babban farin kursiyi, shi ne ka bada gaskiya ga Isa Almasihu da ya zama Ubangijinka da mai ceton ka zaka sami tsira. A cikin Ayyukan Manzani sura 16:31-34, ma’aikacin gidan yari ya sami tsira ta wannan hanya tare da iyalin sa. Ba da gaskiya ga Isa Almasihu Yesu yanzu, yi addu’a ka roka gafara zunuban ka, da wannan a shirye ka ke domin tsira daga shrin saduwarda ba a iya kauce wa.

Idan ta dalilin karanta wannan karamin kasida ka yi kudirin imani da Isa Almasihu Yesu ya zama mai ceton ka; sai ka rubuto mana domin taya ka farin cikin da addu’a.